



An yi kunkuru da zomo a dawa.

Zomo na da saurin tafiya.


Kunkuru kuma na tafiya da hankali.



Zomo na da rigima ka saurin shi.

Ya ce su yi tsere da kunkuru.

Kunkuru ya amince da tsere.



Kunkuru ba ya saurin tafiya kamar zomo. Amma kunkuru ya fi zomo hikima.




Kunkuru ya ce su hau

tudun dutse.

Su yi tseren sauka daga

tudun dutse.


Zomo ya amince.




Zomo ya hau tudun dutse da sauki.

Da kyar kunkuru ya isa saman dutse.

Dabbobi na jira a ƙasa.






Zomo ya shirya.

Kunkuru ya shigar da

kansa da ƙafafunsa.


Tsere ya fara.



Kunkuru ya gangaro da sauƙi kamar dutse.

Ya fitar da kansa da ƙafafunsa.

Da kyar zomo ya isa ƙasa.



Kunkuru ya yi nasara a tsere.

Hikimar kunkuru ta fi saurin zomo.